| JUMHURIYYAR MISRA TA LARABAWA | 16 Ramadhan, 1444 |
| --- | --- |
| MA'AIKATAR ADDININ MUSULUNCI | 7 Afrilu, 2023 |

(١)

# NATSUWA DA KWANCIYAR HANKALI A KWANAKI GOMAN ƘARSHEN RAMADAN

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **(Su ne waɗanda suka yi imani, zukatansu kuma suka sami cikakkiyar natsuwa sakamakon zikirin Allah..)** [al- Ra'ad: 28]. Ina shaida cewa lallai babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina kuma shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammad bawan Allah ne kuma Manzonsa, Ya Allah Ubangiji ka ƙara masa tsira da aminci da albarka, shi da alayensa da sahabbansa, da duk wanda ya bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, Bayan haka:

Lallai natsuwa, da kwanciyar hankali haske ne, da kuma samun yaƙini da jin daɗi a cikin zuciya, Allah Maɗaukakin Sarki yana sanya su ne a cikin zukatan bayinsa muminai, ba ya yarda damuwa ta yi masu nauyi, ba kuma ya yarda fitintunu su girgiza su, ko bala'o'i su raunata su, hasali ma masu waɗannan zukatan imani, da ƙarfi, da tabbata akan gaskiya suke ƙara yi, Allah mai girma yana cewa: **(In ma ba ku taimaka wa Annabi Muhammadu (SallalLahu alaiHi wa sallam) ba, to ku sani tabbas Allah ya riga ya taimake shi a lokacin da kafirai suka fitar da shi daga garin Makka su biyu, lokacin da suke cikin kogo da yake faɗa wa abokinsa cewa: kada ka damu, lallai Allah yana tare da mu, sai Allah ya saukar masa da natsuwa, ya kuma ƙarfafe shi da rundunar da ba ku iya ganinta, ya kuma sanya kalmar kafirai ta zamo a ƙasa, lallai kalmar Allah ita ce a sama, tabbas Allah cikakken mabuwayi ne, mai kuma cikakkiyar hikima) [at- Tauba: 40].**

Lallai Alƙur'ani mai girma ya yi matuƙar muhimman natsuwa da kwanciyar hankali, inda waɗannan ma'anoni suka zo a cikin siyaƙin magana akan lokutan tsanani, da tsoro da zukata suka tsinci kawunasu cikin razana da tsoro, a irin waɗannan lokuta ne kuma Allah yake saukar da natsuwa da kwanciyar hankali a cikin zukatan masu jin tsoronsa, suna yi masu albishir da cewa Allah yana tare da su, taimakonsa da ƙarfafawarsa suna tare da su, Allah Maɗaukakin Sarki yana faɗi game da ranar yaƙin Badar cewa: **(Allah Mai girma ya tunatar da muminai ni'imar nasarar da ya ba su a yaƙin Badar, lokacin da suka yi haƙuri, sai ya tabbatar masu da cewa: lallai shi ne ya taimake su a wajen yaƙin, lokacin da suke da ƙaranci adadi, da kuma ƙarancin makamai, ya kuma neme su da su yi masa biyayya da ɗa'a; domin su gode masa akan wannan ni'ima.. Nasarar ta kasance ne lokacin da Manzon Allah (SallalLãhu alaiHi wa sallam) ya ce wa muminai: shin taimakon da Ubangijin ku ya yi maku na sauko da Mala'iku dubu uku daga gare shi; domin su ƙarfafe ku, bai isa ya kwantar maku da hankali, ya kuma sanya maku natsuwa ba?. Ey, lallai wannan ƙari ya isa ya sanya zukatanku su natsu, idan kuka yi haƙuri a wannan yaƙi, kuka kuma yi riƙo da tsoron Allah, idan maƙiyanku suka zo maku nan-take Ubangijinku zai ƙara maku Mala'iku adadin su ya kai dubu biyar da zai saukar da su daga wurinsa domin su ƙarfafe ku.. Allah Mai girma bai sanya wannan ƙari na Mala'iku ba, face su zama maku albishir ne na nasara; saboda zukatanku su natsu, amma fa babu wata nasara sai wadda ta zo daga Allah, wanda shi ne yake sanya komai a inda ya dace da shi, shi ne kuma yake tsara bautar bayinsa muminai) [Ali Imran: 123 -126],** game da

ranar yaƙin Hunaini kuma Allah yana cewa: **(Ya ku muminai, lallai Allah ya taimake ku akan maƙiyanku a wurare masu yawa saboda ƙarfin imaninku, lokacin da yawanku ya ruɗe ku a yaƙin "Hunaini" sai Allah ya bar ku da kawunanku a farko, sai yawan naku ya gaza tsinana maku komai, maƙiyanku suka yi galaba akanku, saboda tsananin tsoro da razanar da kuke ciki ne duniya ta yi maku ƙunci, kuka rasa hanyar da za ku bi ku tsira daga wannan yaƙi, ko samun tsira mai daraja, mafi yawanku ba su sami hanyar tsira da rayukansu ba sai ta hanyar gudu, sai kuka ranta a na kare cikin karaya, kuka bar Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) tare da wasu muminai 'yan kaɗan. Daga nan ne kuma taimakon Allah ya riske ku, sai ya saukar wa Manzonsa (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) da natsuwa, ya kuma cika zukatan muminai da ita, ya ƙarfafe ku da ƙarin rundunarsa ta mala'ikun da suka tabbatar da diga- diganku, ku ba ku iya ganinsu ba, sai kuka sami nasara.. ya kuma ɗanɗana wa maƙiyanku ɗacin karaya da rashin samun nasara, lallai wannan shi ne sakamakon kafirai a duniya)** [al- Tauba: 25 - 26].

A ranar Hunaini lokacin da sahabbai (Allah ya ƙara yarda da su) suka ga cewa kaman akwai ƙwara a cikin sharuɗɗan sulhun, wannan abu ya yi masu zafi, sai Allah mai girma da ɗaukaka ya saukar masu da natsuwa da kwanciyar hankali a cikin zukatansu, suka sanyaya zukatan nasu, suka kuma ƙara samun tabbata, inda kalmar "natsuwa" sai da ta maimaitu har sau uku a cikin littafin Allah saboda bayyana abin da ya keɓanci wannan rana, Allah mai girma yana cewa: **(Shi ne Allah wanda da ya saukar da natsuwa a cikin zukatan muminai; domin su ƙara samun tabbaci da yaƙini**

**akan tabbaci da yaƙinin da suke da shi, kuma Allah kaɗai ne yake da rundunar sammai da ƙasa, shi yake tsara al'amurransu kamar yadda yake so, lallai ilimin Allah ya mamaye komai, shi ne kuma mai cikakkiyar hikima a wajen zartad da dukan sha'ani)** [al- Fathi: 4], haka ma mai girma da ɗaukaka yana cewa: **(Lallai tabbas Allah ya yarda da muminai a lokacin da suke yi maka mubaya'a da zaɓin kansu a ƙarƙashin bishiya, ya kuma san abin da yake cikin zukatansu na yin abu saboda Allah, da cika alƙawari ga saƙon da ka zo da shi, sai ya saukar masu da natsuwa, saboda kuma gaskiyarsu wajen mubaya'a da cika alƙawarin sulhun ne Allah ya yi gaggawar ɗaukaka darajarsu)** [al- Fathi: 18], Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Lokacin da waɗanda suka kafirce suka sanya taurin-kai irin na zamanin jahiliyya a cikin zukatansu, sai Allah ya saukar wa Manzonsa da muminai da wata natsuwa, ya kuma lizimta masu kalmar da za ta katange su ga barin shirka da azaba, da ma kalmar tasu ce, su ne kuma suka fi cancanta da ita, lallai ilimin Allah ya game komai)** [al- Fathi: 26].

Babu shakka cewa lallai ambaton Allah mai girma da buwaya, da hararo girmansa, da jin cewa yana tare da mu, su ne manyan dalilan samun natsuwa da kwanciyar hankali, da su ne zukata suke yin haske, su sami hutu, su kuma rayu, Allah mai girma yana cewa: **(Su ne waɗanda suka yi imani, zukatansu kuma suka sami cikakkiyar natsuwa sakamakon zikirin Allah..)** [al- Ra'ad: 28], Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya ce: **(Misalin wanda yake ambaton Ubangijinsa, da wanda ba ya ambaton Ubangijinsa, kaman rayayye ne da matacce)**, haka ma Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana

cewa: **(Mutane ba su taɓa taruwa a cikin ɗaya daga cikin ɗakunan Allah, suna karanta littafin Allah, suna nazarinsa a tsakaninsu ba, face an saukar masu da natsuwa, rahama kuma ta lulluɓe su, mala'iku kuma sun yi haba- haba da su, Allah kuma ya ambace su ga waɗanda suke a wurinsa)**.

Lallai Allah ya umurce mu da yin natsuwa da kwantar da hankali a cikin dukan ibadun da muke yi, domin a duk sanda natsuwa ta sauka a cikin zuciya, sai gaɓoɓin su sami hutu, sai tsoron Allah ma ya sauka, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Idan kun ji an tayar da iƙama, ku tashi ku tafi wurin sallah cikin natsuwa da kwarjini, kada ku yi gaggawa, duk abin da kuka samu ku sallata, abin da ya wuce ku kuma ku cika)**, haka ma (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Ya ku mutane, ina horonku da yin riƙo da natsuwa, ku sani cewa lallai biyayya ba da gaggawa ake yinta ba)**, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya ga an wuce da wata janaza cikin gaggawa, sai ya ce: **(Ya kamata a ce kuna da natsuwa).**

***

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da aminci su tabbata ga cikamakin Annabawa da Manzanni, shugabanmu Annabi Muhammadu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam), da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

Lallai duk wanda ya ɗanɗani zaƙin natsuwa da kwanciyar hankali a cikin watan Ramadan, a lokacin da ya kyautata dangantakarsa da Allah mai girma da buwaya, ya kusance shi da nau'o'in ibadu da ayyuka na gari, to kuwa lallai ya kamata a ce ya ƙara zage- dantse a goman ƙarshe na watan Ramadan; ya ribaci falala da albarkar da suke ciki, ya

sami cikakken hutu da jin daɗi wa zuciyarsa, ganin cewa Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana ƙara himma da ƙoƙari a cikin waɗannan kwanaki goman, Sayyida A'isha (Allah ya ƙara yarda da ita) ta ce: **(Idan aka shiga kwanaki goman ƙarshe, Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yakan ƙara ɗamara, ya kuma tashi iyalansa)**, haka ma (Allah ya ƙara yarda da ita) ta ce: **(Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yakan ƙara ƙoƙari a kwanaki goman ƙarshe na watan Ramadan da bai yi a waninsa)**.

Lallai muna ƙara tabbatar da cewa, taimako da jinƙai, da wadata talakawa da miskinai suna cikin ainihin ibada, sawa'un ta hanyar fitar da zakka ne, ko kuma ta hanyar yawaita yin sadaka, ko kuma ta hanyar gaggauta fitar da zakkar kono, da yalwata wa mabuƙata, ta yanda soyayya da ƙauna za su mamaye rayuwar al'umma, al'umma ta zama kaman jikin ɗaya, kaman yanda Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yake cewa: **(Misalin muminai wajen soyayyar junansu, da jinƙan junansu, da tausayin junansu, kaman jiki ne da idan wata gaɓa da cutu, sai sauran jiki ya kamu da rashin barci gami da raɗaɗin ciwo),** haka ma (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Duk wanda ya yaye wa Musulmi wani baƙin- ciki, daga cikin baƙin cikin duniya, Allah zai yaye masa baƙin- ciki daga cikin baƙin- cikin ranar alƙiyama, duk wanda ya sauƙaƙa wa talaka da yake cikin matsananciyar buƙata, Allah zai sauƙaƙa masa a duniya da lahira, duk wanda ya suturta Musulmi, Allah zai suturta shi a duniya da lahira, lallai Allah zai taimaki bawansa, matuƙar bawan yana taimakon ɗan uwansa).**

(٧)

Ya Allah ka sanya muna cikin bayinka da ka ‘yanta su ga barin wuta, ka kuma yi masu rahama, ka kiyaye ƙasashenmu, da dukan duniya baki ɗaya.